

## ABOUT CITAD

CITAD (www.citad.org)
Is A Capacity Building Civil Society Organization Whose Activities Covers Research, Advocacy, Training And Publicity In All Areas Of Icts.
Its Vision Is; A Knowledge-based Democratic Society Free Of Hunger While Its Mission Is; Using ICTs To Empower Citizens For A Just And Knowledge-based Society That Is Anchored On Sustainable And Balanced Development.


**MAIN OFFICE:**
3rd Floor, NISTF Building, No.1A, Social Insurance Road, Behind Trade Fair Complex, Zaria Road, Kano. P.O. Box 10210, Kano, Nigeria.
GSM: 0800-68078282, 080-54362931, 070-33427467 •
E-mail: info@citad.org, Citadev@gmail.com, citad4peace@citad.org,
Website: www.citad.org, www.citad4peace.org.ng


**BAUCHI OFFICE:**
NUJ Secretariat, Opposite Reinsurance House, Ahmadu Bello Way, Bauchi State.
GSM: 08064867312


**CITAD**.....*A Knowledge-Based Democratic Society Free of Hunger*


*Tsarawar*
Cibiyar Bunƙasa Fasahar Sadarwa Da Ci Gaban Al'umma (CITAD)
Tare Da
Gudummawar Ƙungiyar ActionAid Ta Najeriya (AAN)


# KUNDIN SAMAR DA CIGABAN GARIN WUDILAWA






CITAD

CENTRE FOR INFORMATION TECHNOLOGY AND DEVELOPMENT

# KUNDIN SAMAR DA TSARIN CI GABAN GARIN WUDILAWA

*Tsarawar*

**Cibiyar Bunƙasa Fasahar Sadarwa Da Ci Gaban Al'umma (CITAD)**
**Tare Da**
**Gudummawar Ƙungiyar ActionAid Ta Najeriya (AAN)**

CITAD

actionaid

UKaid from the British people





## ABUBUWAN DA KE CIKI


Shafin Farko....................i
Jadawali....................ii
Godiya....................1
Gabatarwa....................2
Manufa....................3
Hanyoyin Da Aka Yi Amfani Da Su....................3
Tsarin Da Aka Yi Amfani Da Shi....................3
Cikakken Bayani Game Da Garin Wudilawa....................3/6
Tarihin Garin Wudilawa....................7/8
Taswirar Garin Wudilawa....................8/10
Yanayin Zamantakewa....................10/11
Lafiya....................11/12
Ilimi....................13/13
Juyawar Yanayin....................13/14
Kadarori....................15
Tantance Matsalolin Da Ke Addabar Garin Wudilawa....................15
Tantance Haƙƙoƙin Mata....................16/17
Take Haƙƙoƙin Ɗan Adam....................18/19
Kalubalen Da Ke Fuskantar Garin Wudilawa A Halin Yanzu....................20/21
Tantance Matsaloli Ta Amfani Da Bishiyar Matsaloli....................22/23
Kungiyoyi da Mutane da Zasu Iya Tallafawa....................24
Tantance Yanayin Karfin Iko (Nazari Kan Waɗanda Keda iko)....................25/26
Tantance Hanyoyin Samun Bayanai....................27
Tsarin da aka Shirya Gudanarwa....................28

# GODIYA

Wallafawar wannan littafi yasamu yiwuwane tareda tallafi daga Sashin Kula da Cigaba na ƙasa da ƙasa na Gwamnatin Birtaniyya (DFID ta hannun ƙungiyar ActionAid Nigeria (AAN). Dole ne a yabawa wannan Cibiya ta ActionAid saboda jajircewa ta wajen Bunƙasa Demokuraɗiyya ta hanyar wayar da Jama'a su fahimci Demokuraɗiya.

Muna godiya ta musamman ga Shugaban Cibiyar Fasahar Sadarwa da Ci gaban Al'umma (CITAD), Y.Z. Ya'u domin kasancewarsa jigo wanda ya bada gudummawa ga kammaluwar wannan Littafi.

Godiyar mu bazata cikaba sai mun yaba da Kyakkyawar fahimta da hadin kai da ma'aikatan CITAD. Haka kuma mun yabawa da ƙoƙari da himmar Malam Ahmad AbdullahiYakasai, da Isyaku Garba' da Abubakar Auyo da Mukhtar Sulaiman Umar da Abdullahi Jido da Harira Abdulrahman wanda suka hana kansu hutu domin tabbatar da kammaluwar wannan Kundi.

Muna miƙa cikakkiyar godiyarmu ga 'Yan kwamitin aiwatar da kundin wannan Gari na Wudilawa da Mai Gari da Dagaci da kuma dukkannin waɗan da suka tallafa wajen gudanar da tsarin shirin wannan kundi, babu shakka zai ingan ta shirin nan gaba.



KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN GARIN WUDILAWA 2016

# GABATARWA

Wannan kundi na cigaban wannan gari yana ɗauke da gabaɗayan bayanai filla-filla da kuma taƙaitattun abubuwan da suka shafi garin Wudilawa da ke ƙaramar hukumar Gaya a jihar Kano a tarayyar Najeriya. Wannan kundi zai zama wata madogara na yin iznawajen tabbatar da gaskiyar al'amura ga jama'ar Wudilawa. Kundin yayi cikakken bayanin garin da mutanensa da kuma albarkatun ƙasa da Allah Ya huwace masa. An tattaro waɗannan bayanai ne daga wajen wasu keɓantattun mutane mazauna garin ta hanyar yin amfani da tsarin waiwaye adon tafiya domin yin bitar abubuwan da suka gudana da kuma tsarin nan na Action Aid wanda ke baiwa kowa damar bayar da gudummawa don tattara da faɗakar da mutane sanin muhimmancin kowa ya shiga a dama da shi a al'amuran zaɓe wanda aka fi sani da (SCEEP).

Tsarin zai zama wani ginshiƙi na aiki tare da wasu garuruwan a ƙoƙarin saita al'umma kan gwadaben da za su rinƙa bibiyar abubuwan da gwamnatoci da wakilansu ke gudanarwa. Haka kuma, wannan kundin zai samar da wata kafa ta yin aiki tare tsakanin al'ummar garin da waɗanda suka zaɓa zuwa matakai daban-daban. An samar da kundin ne ta bin managartan tsare-tsare da wannan ƙungiya ta yi a baya, aka tattaro ƙwararru suka yi aiki ƙarƙashin inuwa ɗaya.

Hanyar amfani da tsarin waiwaye adon tafiya na yin amfani da cikakken bincike kamar binciko dangantakar mahukunta da haƙƙoƙin al'umma musamman mata da gano abubuwan da ke yi wa garin barazana da binciko ƙungiyoyi da mutanen da za su iya tallafawa da fahimtar hanyoyin sadarwa da al'ummar garin ke amfani da su da kuma matsalolin da suke ci musu tuwo a ƙwarya.

Domin cimma nasara abubuwan da aka ambata a sama, ActionAid ta aiwatar da tsarin waiwaye adon tafiya a garin. Ta amfani da sassa bakwai na tsarin tantancewar bayanai. Bayanan da aka tattara za su zama ginshiƙi na ƙarfafa gwiwa wanda zai ciyar da garin gaba yadda ake buƙata.

**MANUFA**

Manyan manufofin wannan kundi su ne kamar haka:

- Gano tare da adana al'amuran da suka shafi garin Wudilawa tare da fitar da wani tsari na shigo da al'ummar yankin don yin aiki tare.
- Zaburar da al'umma wajen neman abubuwan cigaban garin daga wakilansu a ɓangarori daban-daban.
- Tallata ƙwarewa da ilimi da kuma abubuwa da garin Wudilawa ke fatan samu a dunƙule domin samun sauƙin bibiya.

## HANYOYIN DA AKA YI AMFANI DA SU

Hanyoyin da aka bi wajen aiwatar da aikin sun haɗa da:

- Tattaunawa tun a karon fari tsakanin dattawan Wudilawa da CITAD.
- Ziyarce-Ziyarce: An ziyarci wurare daban-daban tare da ganawa da mutanen na garin na tsawon kwanaki domin samun cikakkun bayanai na ɓangarori bakwai na waiwaye adon tafiya (Reflection Action).
- Taron tantancewa da rubuta rahoton abubuwan da aka gano.

## TSARIN DA AKA YI AMFANI DA SHI

An yi amfani da abubuwa daban-daban wajen tantance ɓangarori bakwai na waiwaye adon tafiya (Reflection Action).

An yi amfani da taswira wajen binciko matsalolin da ke addabar garin.

An yi amfani da jerin gwanon haƙƙoƙin ɗan'Adam wajen gano haƙƙoƙin al'ummar Wudilawa.

Jera abubuwa mafi sauƙi ya taimaka wajen tsara al'amuran da suka fi muhimmanci bi da bi waɗanda al'ummar garin suka gano.





An yi amfani da bishiyar-matsaloli domin fahimtar abubuwan da suka haddasa matsalolin da tasirinsu da kuma tattaunawa mai zurfi a kansu.

An yi amfani da salon tantance cibiyoyi da mutanen da za su iya bayar da tallafi domin gano waɗanda za su iya hoɓɓasa kuma suke da ikon kawo canji ga abubuwan da garin ke buƙata.

An yi amfani da tsarin zane na Venn domin a tantance matakin tasirin da cibiyoyi da mutanen da za su iya taimakawa da alaƙarsu da garin.

An yi amfani da salon yanar-gizo wajen tantance haƙƙin mata.

Tsarin tantance matsaloli ya fitar da abubuwa daban-daban da ka iya cutar da garin.

Zanen hanyoyin sadarwa ya tantance hanyoyin da al'ummar garin ke isar da saƙo tsakaninsu da sauran garuruwa da waɗanda za su iya bayar da gudummawa. A ƙoƙarin aiwatar da tantance abubuwa daban-daban, an tattauna da kowa da kowa, an tattauna a ƙungiyance don a yi tambayoyi da kuma yin bincike mai zurfi domin a samu tantancewa mai inganci.

## Cikakken Bayani Game Da Garin Wudilawa

| | |
|---|---|
| Sunan Gari: | Wudilawa |
| Karamar Hukuma: | Gaya |
| Jiha: | Kano |
| Adadin Al'umma: | 97,375 (Maza:47,754 Mata:49,621) |
| Adadin Magidanta: | 12,797 |
| Adadin Dattijai Maza Magidanta: | 22,330 |
| AdadinDattijai Mata Magidanta: | 342 |
| Adadin matasa Magidanta: | 152 |

AJUJUWAN SHEKARUN AL'UMMAR GARIN

| | |
|---|---|
| Shekara 0 zuwa 5 | 13,475 |
| Shekara 6 zuwa 10 | 13,100 |
| Shekara 11 zuwa 18 | 7,006 |
| Shekara 19 zuwa 30 | 10,122 |
| Shekara 31 zuwa 40 | 11,570 |
| Shekara 41 zuwa 50 | 21,683 |
| Shekara 51 zuwa 60 | 10,150 |
| Shekara 61 zuwa 70 | 9,135 |
| Shekara 70 zuwa sama | 1134 |
| Adadin Jama'ar Garin Gabaɗaya | 97,375 |

Sana'ar Mutanen Garin: Nomada Kanana Kasuwnci

Kayayyakin abincin da aka fi sayarwa: Gero, Wake, Masara da

Dawa

Kuɗaɗen da ke shigowa/Kuɗaɗen da ake kashewa

Matsakaicin abin da ke shigowa mutum a shekara: N250, 000

Matsakaicin abin da mutum yake kashewa a shekara: N250, 000

Matsakaicin abin da ma'aikaci yake samu a kullum : N600,**000**

Matsakaicin abin da ma'aikaci yake kashewa a shekara N6000,000

## Lafiya

Asibitin da ke akwai a garin nada tazarar kilomita ɗaya daga cikin garin, akwai ƙwararrun ma'aikatan lafiya a asibitin amma dukkanninsu maza ne. idan annoba ta ɓarke a garin, jama'ar garin na sanar da mahukunta musamman dagaci da masu unguwanni domin kawo ɗauki domin sune mutanen dake kusa da jama'a. Ana ɗigon rigakafi a asibitin, da kuma tattara bayanai akan duk wata cuta da aka gano don yunƙurin kawar da ita. An tattara wannan bayani ne daga gurin ɗaya daga cikin ma'aikatan lafiya yayin samar da wannan kundi. Kananan yara 'yan ƙasa da shekara biyar su suka fi saurin kamuwa da cututtuka. Yawanci mata masu juna biyu kan haihu a gida tare da taimakon ungozomomi na gargajiya





waɗanda suka sami horon karɓar haihuwa.Idan haihuwar tazo da matsala kuma ungozomomin kan tura matan zuwa asibiti don haihuwa a can amma hakan bai fiye faruwa ba.

Al'ummar garin sun lura cewa an ɗan sami cigaba akan abubuwan da suka shafi lafiya a garin musamman yadda aka yi gyran ɗakunan dake asibitin garin, wani lokacin kuma a bayar da magani kyauta.

## Ilimi

Makarantu: makarantar firamaren garin na da tazarar mita 20 zuwa 500 (tafiyar minti 10 zuwa 15)

| | | | |
|---|---|---|---|
| Adadin yaran da suka shiga makaranta a halin yanzu: 1283 | Adadin yara maza: 1190 | Adadin yara mata: 93 | Adadin 'yan ƙasa da shekara 5: |
| | Adadin yara 'yan shekaru 6 zuwa 10: 13,345 | Adadin 'yan shekaru 11 zuwa 15: 1562 | Adadin 'yan shekaru 16 zuwa 20 (idan ana buƙata) 203 |

| | |
|---|---|
| Adadin waɗanda suka kammala firamare 7,065 | Adadin yara maza:,500 |
| | Adadin yara mata:265 |
| Adadin waɗanda suka kammala sakandare a garin:450 | Adadin yara maza:200 |
| | Adadin yara mata:150 |
| Adadin waɗanda suka kammala makarantar gaba da sakandare:170 | Adadin yara maza:160 |
| | Adadin yara mata:10 |
| Adadin waɗanda ba su taɓa zuwa makaranta ba: 6,064 | Adadin yara maza:20,761 |
| | Adadin yara mata:5,000 |
| Adadin yaran da suka daina zuwa makarantar firamare: 18,801 | Adadin yara maza:7,301 |
| | Adadin yara mata: 11,500 |
| Adadin yaran da suka daina zuwa makarantar sakandare: 9,000 | Adadin yara maza: |
| | Adadin yara mata: |



# TARIHIN GARIN WUDILAWA

Mazaɓar Wudilawa ɗaya ce daga cikin mazaɓu 10 dake ƙaramar hukumar Gaya a jihar Kano. Garin na yamma maso kudancin garin Gaya, shelkwatar garin na garin Gungura. Haka nan Garin nada faɗi da tsahon kilomita 13 da kuma yawan al'ummar da yakai 97,000 a jadawalin ƙidayar shekara 2006. Garin yayi iyaka da ƙaramar hukumar Wudil daga Arewa da Yamma. Yayi iyaka da mazaɓar Kademi daga Kudu da kuma Shagogo daga Gabas.

Garin Wudilawa gari ne da yake tun shekarar 1915 an kuma yi amannar cewa asalin garin ya samu daga wani mutum mai suna Alu Ramata wanda shi ne mazauni na farko a wannan gari na Wudilawa. Mutumin ya zo ne daga Sokoto inda ya fara zama a garin Kanta a ƙaramar Hukumar Warawa da kuma Wudil daga baya kuma ya koma Cukulo wanda shi ne garin Wudilawa a yanzu. Yawancin sana'o'in mutanen Wudilawa su ne Noma, Kasuwanci, Kira da sauransu.

Wanda ke riƙe da sarautar garin Wudilawa shi aka fi sani da suna Sarkin Wudilawa. Malam Isah shi ne sarki na farko a wannan gari, sannan Malam Idrisu, sannan Malam Ibrahim, sannan Malam Halliru wanda wata 6 kurum yayi a mulikin garin ya rasu. Sai Malam Idrisu ya ƙara komawa kan mulkin garin. Bayan ya rasu ne ɗansa Bello Idrisu ya gaje shi, a halin yanzu shi ne Sarkin Wudilawa. An haifi Bello Idrisu a Wudilawa haka kuma tun a shekarar 1966 yake kangadon sarautar garin. Allah ya albarkaci garin da al'umma da dama. Akwai masu unguwanni 14 da dagaci guda 1 da kuma ƙananan asibitoci guda 4, biyu daga ciki na karɓar haihuwa ne da kula da ƙananan yara, asibitocin na Amaryawa da Gungara amma ba'a kwanciya. A waɗannan asibitoci ake awon ciki da kula da lafiyar ƙananan yara yan ƙasa da shekara 5. Akwai makarantun firamare guda 4 da islamiyoyi guda 5 a gurare daban daban a wannan mazaɓar wadanda ke bayar da ilimin zamani da na addini domin haɓaka ilimi a wannan gari.



KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN GARIN WUDILAWA 2016

Duk da irin albarkar da Allah ya yiwa wannan gari na jama'a, garin nada ƙarancin ababan more rayuwa kamar wutar lantarki, hanyoyi, ƙarancin kayayyakin kula da lafiya, rashin makarantar sikandire da kuma ƙarancin ruwan sha. Wannan garin bai da wasu sanannun albarkatun ƙasa. Garin na fama da matsanancin ambaliyar ruwa duk shekara sakamakon mamakon ruwan saman dake malala zuwa kogi kusa da garin.

# TASWIRAR GARIN WUDILAWA

Matasan garin ne suka samar da taswirar, inda mata da dattijai da samarin garin suka halarci taron samar da tasawirar. Hakan kuwa shi ya bayar da damar samun cikakken bayanin garin, matsalolinsa da damarmakin dake garin a bayane da kuma a cikin hoto. Abubuwan da aka gano a yayin zanen taswirar sun haɗa da albarkatun ƙasa da ababan more rayuwada kuma ayyukan jama'ar gari. Taswirar ta nuna canje-canjen da aka samu a baya da waɗanda ake fatan samu nan gaba. Taswirar ta nuna gidaje, makaranta, masallaci, asibiti, kasuwa, makewayi, fanfuna, rijiyoyi da kuma guraren da ke fuskantar barazana sakamakon anbaliyar ruwa a cikin garin.

## MATAN GARIN KE TATTAUNA BATUTUWA DABAN-DABAN KAN TASWIRAR GARIN



Kungiyoyin Mata Yayin Samar Da Taswirar Garin




Wasu Daga Cikin Matasan Da Suka Halarci Taron Samar Da Wannan Kundi





## TASWIRAR GARIN WUDILAWA






### YANAYIN ZAMANTAKEWA

Wudilawa nada adadin al'umma 97,375 (47, 754 maza da 49, 621 mata) da magidanta 12, 797. Akwai 22,3300 Dattijai maza magidanta da 342 Dattijai mata magidanta sai kuma 152 kananan yara magidanta a garin.

'Yan shekaru 0 zuwa 5, da shekaru 6 zuwa 10 da shekaru 41 zuwa 50 su suka fi yawa a garin. (Duba Jadawalin Shekaru domin cikakken bayani) Bugu da ƙari, jama'ar garin Wudilawa yawanci su manoma ne, inda suke noman Dawa, Gero, Masara, Tattasai da kuma kiwo (kiwon Shanu, Awaki da Tumaki). Matsakaicin abin da ke shigowa mutum a shekara ya kai N600,000 (Matsakaicin abin da ke shigowa mutum a kullun yakai N250) Haka ma, Matsakaicin abin da mutum yake kashewa a shekara ya kai N6000,000 (Matsakaicin abin da mutum ke kashewa a kullun ya kai N500). A wani bangaren kuma matsakaicin abin da ke shigowa ma'aikaci a shekara ya kai N600,000 (matsakaicin abin da ke shigowa ma'aikaci a kullun ya kai N500)



## YANAYIN ZAMANTAKEWA

Garin Kademi na cikin ƙaramar hukumar Gaya, gari ne dake da nisa daga garin Kano, garin na da yawan al'ummar da yakai 359,000 (10,100 maza da 358,000 mata). Babu wata ƙididdiga da ta nuna yanayin Jagoranci a tsakanin iyalai a wannan gari. Yara dake tsakanin shekaru 0 zuwa 5 su suka fi yawa a wannan garin (duba ajujuwan shekarun al'ummar garin domin ƙarin bayani).

Bugu da ƙari, yawancin al'ummar Kademi manoma ne da ƙananan 'yan kasuwa. Manoman kan noma Gero, da Dawa da Rogo da Kayan Miya da N153, 000 a matsayin matsakaicin kuɗin shiga a shekara ga magidanci. Da kuma N300 a matsayin matsakaicin kuɗin kashewa a kullun ga magidanci.Yawan mazauna garin kan kashe yawancin kuɗaɗen da suke samu a kullun saboda noman kayan miyar da suke yi.




## LAFIYA

Akwai ƙaramin asibiti dake aiki halin yanzu a garin wanda gwamnati ta gina.Asibitin nada ma'aikata guda 6, da kuma magunguna da kayayyakin kula da lafiya da ba a rasa ba. Sai Dai mutanen garin kanyi tafiyar kilomita 20 zuwa babban asibitin garin Gaya domin abin daya shafi kula da lafiyarsu kamar lamarin da ya shafi haihuwa musamman idan haihuwa tazo da tangarɗa. Idan kuma aka sami matsalar ɓarkewar annoba, akan duba wanda cutar ta shafa a asibitin, wasu lokutan kuma akan tura marasa lafiyar asibitoci kwararru idan buƙatar hakan ta taso.

Haka kuma, mata masu juna biyu kan je asibitin domin duba lafiyarsu, wani lokacin kuma akan nemi gudumowar ungozomomin gargajiya da aka yi musu horo idan haihuwa tazo da matsala musamman idan lokaci ya ƙurace yadda ba za a iya





zuwa babban asibitin garin Gaya ba duba da lokacin da za a bata a hanya kafin a isa can. Sai dai jama'a na ƙorafin ƙarancin ma'aikatan lafiya mata a asibitin.

Kodayake Wudilawa ta sami cigaba a bangaren lafiya saboda raba gidajen sauro da akayi don yaƙar zazzabin maleriya. Haka kuma ana ɗigon maganin shan inna da ƙyanda da zazzaɓin shawara akai-akai.



## ILIMI


Akwai makarantun firamare da Islamiyya guda 4 a garin. Gwamnati ce ta gina makarantun 3, wannan shi ke nuni da cewa akwai damar samun ilimi a garin. Ana baiwa yara maza da mata dama iri ɗaya wajen bayar da ilimi. Hakan ya samu ne saboda gudumowar wasu shugabanni a garin.
Bugu da ƙari, Adadin mutane 7,065 sun kammala firamare a garin,

Domin tantance ingancin ilimi a garin Wudilawa an yi amfani da kundin da yake ɗauke da haƙƙoƙin ciyar da ɗalibi gaba (Promoting Rights in School Charter). Haƙƙin ciyar da ilimi gaba a makarantu ya ta'allaƙa kan haƙƙoƙi guda goma da aka rairayo daga Tsarin Shari'a na ƙasa (National Legal Instruments) (watau kamar kundin tsarin mulki da yarjejeniyar haƙƙoƙin ɗan'Adam na ƙasa da ƙasa).

An yi amfani da shirin PRS domin tantance haƙƙoƙin ilimi a garin. Manufar da PRS ke son ya cimma ita ce shigo da al'ummar ƙasa domin tabbatar da ilimi mai inganci sannan a gane fahimtar 'yan ƙasa a wuraren da suke rayuwa. Inda a tsarin lamba 1 ce mafi ƙaranci, 5 kuma lamba mafi girma. Ga haƙƙoƙin:

| Yarjejeniyar PRS | Tantancewa (1 mafi ƙaranci, 5 mafi girma) |
|---|---|
| Haƙƙin samun kyakkyawan ilimi kuma kyauta | 3 |
| Haƙƙin rashin nuna wariya | 3 |
| Haƙƙin samar da isassun kayayyakin more rayuwa | 3 |
| Haƙƙin samar da wajen zama marar haɗari | 2 |
| Haƙƙin samar da ƙwararrun malamai | 5 |
| Haƙƙin samar da tsarin koyarwar da ya dace | 2 |
| Haƙƙin sanin 'yancin kai | 4 |
| Haƙƙin a dama da mutum a wajen ɗaukar mataki | 1 |
| Haƙƙin samar da makaranta marar ƙunbiya-ƙunbiya | 1 |
| Haƙƙin samar da ingantacciyar koyarwa | 3 |

Jadawali na sama yana nuni da cewa yara ba sa shiga a dama da su a wajen ɗaukar mataki kan wani abu da ya shafi al'umma. Haka kuma samun isassun kayayyakin more rayuwa, sannan ga tauye musu haƙƙi na samun ingantacce kuma kyakkyawan ilimi kyauta da kuma haƙƙin samar musu da ingantacciyar koyarwa.




## JUYAWAR YANAYI

An danganta garin Wudilawa da ruwan sama, yadda ake samun ruwan sama tsakanin watan Mayu zuwa oktoba. Lokacin rani na farawa ne tsakani watan Nuwanba zuwa Fabreru. Milmita 200 ne mafi kusan samun ruwa. Jadawalin da ke biye ya nuna yadda yanayin ya karkasu da kuma yadda ayyukan suke gudana a tsakanin waɗannan lokutan. Lokutan samun ruwa a shekara da aikin noma daban daban da al'ummar wannan gari ke gudanarwa.





Yanayin Wudilawa a Tsawon Shekara




Karin haske: VH ƙwarai da Gaske H ƙwarai M Matsakaici L ƙasa VL ƙasa Sosai



Al'ummar garin ke zanen Jadawalin Yanayin Wudilawa na Tsawon Shekara




## KADARORI

Babu wani takamaimai adadin mutanen da suka mallaki gonaki ko ƙananan sana'o'i, amma tattaunawar da akayi da mambobin samar da kundin ya nuna cewa da yawa daga cikin mazajen garin na da gona, haka kuma Mata sun fi 'yan uwansu maza sana'o'i da kasuwanci. Kalilan ɗin mata kan mallaki gonaki tare da samun amfanin gona daga gurin mazajensu.




TANTANCE MATSALOLIN DA KE ADDABAR GARIN WUDILAWA

Matsalolin da aka gano a wannan gari sun haɗa da:

I. Ambaliyar ruwa sakamakon mamakon ruwa sama da kuma yanayin garin
II. Hanyoyin da suka haɗa garin: lokacin mamakon ruwa ƙananan motoci basa iya shiga garin saboda rashin kyan hanya.
III. Hanya: an taɓa yinƙurin faɗaɗa hanyoyin da suka haɗa gonakin garin, amma jama'a sun samar da wasu dabaru na rage matsalolin yadda suke tafiya a ƙungiyance zuwa gonakinsu.

Matsalar ambaliyar ruwa ita ce aka bayyana matsalar da tafi ci musu tuwo a ƙwarya, kuma matsalace da ake fama da ita duk shekara. Al'umma sun bayyana cewa matsalar na jawo asarar rayuka da dukiyoyi wanda ya haɗa da asarar amfanin gona dana dabbobi. Wasu daga cikin jama'ar gari sun yi ƙoƙarin ziyartar wasu hukumomin domin neman taimakon su wajen shawo kan waɗannan matsaloli.





## **TANTANCE** HAKKOKIN **MATA**

A garin Wudilawa al'ada batayi tasiri ba wajen tauye haƙƙoƙin mata ba , haƙƙoƙin mata a fayyace suke a cikin Al'ƙurani mai Girma. Ana ɗaukan haƙƙoƙin mata daga cikin kyawawan aikace-aikacen da addinin musulunci ya tanadar. Addini ya fayyace cewa mata zasu iya mallakar kadarori, su gaji kadarori su kuma shiga a dama da su a harkokin kasuwanci.

Akawaialadu da ɗabi'u da suka cuɗanya a cikin al'umma kamar su auren wuri, hana damar samun ilimi, hana gado ga matan da mazajen su suka mutu da kaciyar mata da kuma damar zaman zawarci. Jama'ar garin sun bayyana cewa duk waɗannan ƙazaman ɗabi'u babu su a garin Wudilawa. Daɗin daɗawa ma addini da al'adun mutanen garin basa goyon bayan waɗannan ƙazaman ɗabi'un na al'ada.

Matsalar kawai da ke damun garin na Wudilawa itace yadda wasu mata ƙalilan ke yin gaban kansu don ɗaukan wani mataki ko gudanar da tarurruka ba tare da tuntuɓar mazajensu ba. Inda zaka samu shugabannin matan jam'iya ke jagorantar irin waɗannan tarurrukan.

Anyi amfani da Jadawalin ayyukan yau da kullun dake tafe domin ƙara faɗaɗa bayanai wajen tantance haƙƙoƙin mata da kuma irin ayyukansu a cikin al'umma. Mutane daban daban ne suka yi tantancewar (Dattijai Maza/Mata, Kananan Yara/Mata) domin kwatanta hanyoyin da mata da yan uwansu maza ke tafiyar da lokutansu .



Matan Garin Wajen Koƙarin Samar Da Jadawalin Ayyukan Yau Da Kullun



Matan garin Wudilawa Yayin Tantance Haƙƙokin Mata





# **TAKE** HAKKOKIN **DAN ADAM**

Duba da rijistar haƙƙin Dan Adam, an gano cewa an takewa mutanen garin Wudilawa wadannan haƙƙoƙin

- Haƙƙin Samun ingantaccen mahalli
- Haƙƙin Samun Abubuwan more Rayuwa
- Haƙƙin Samun Kayayyakin Aiki
- Haƙƙin Samun Ingantaccen Ilimi
- Haƙƙin Samun Abinci
- Haƙƙin ingantacciyar lafiya
- Haƙƙin Samun ingantacciyarRayuwa

Waɗannan haƙƙoƙi nada alaƙa da matsalolin da suke damun wannan garin.

Mutanen garin Wudilawa sun yi amannar cewa an tauye musu haƙƙoƙinsu na abubuwan more rayuwa kamar wutar lantarki, hanyar mota, ingantaccen mahali da ingantaccen ruwan sha. Haka kuma an tauye musu haƙƙin ingantacciyar lafiya saboda rashin ma'aikatan lafiya mata a garin da ƙarancin ɗakunan shan magani.



Jama'ar Garin Wajen Tantance Haƙƙoƙin Dan'adam

# LISSAFIN HAKKOKI

| Jihar /LRP | KANO | | | KARAMAR HUKUMA | GAYA | | GARI | | WUDILAWA | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| Rashin cancanta/ cancanta a samu (mata, yara, talakan da ba shi da fili ko rukunin jama'ar da aka gano) | Adadin waɗanda suka cancanci su samu a yankin da aka yi shirin | | Al'amari | Abubuwan da suka haddasa | Haƙƙoƙin da aka tauye | Kundin tsarin mulki/ policy entitlem-ent | Adadin waɗanda suka cancanci su samu damar da suke neman haƙƙinsu a farkon fara shirin | | Waɗanda nauyin yin aikin ya hau kansu | Sauran muhimman masu ruwa da tsaki |
| | Namiji | Mata | | | | | Namiji | Mata | | |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 47,754 | 49,621 | Lafiya | Rashin ma'aikatan lafiya mata | Hakkin ingantacciyar lafiya da ingantacciyar rayuwa | UDHR da Kundin Tsarin Mulkin ƙasa | 47,754 | 49,621 | Majalisar ƙaramar hukumar Gaya, Ma'aikatar lafiya ta jiha da hukumar samar da lafiya | NGOs |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 47,754 | 49,621 | Kayayyakin aiki a makarantu | | Haƙƙin ingantaccen ilimi | UDHR da Kundin Tsarin Mulkin ƙasa | 47,754 | 49,621 | Majalisar ƙaramar hukumar Gaya, Ma'aikatar Ilimi ta Jiha da KSSSMB | |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 47,754 | 49,621 | Ambaliyar ruwa | | Haƙƙin ingantaccen Mahalli | UDHR da Kundin Tsarin Mulkin ƙasa | 47,754 | 49,621 | Majalisar Karamar Hukumar Gaya, Ma'aikatar Mahalli da HJRBA | Ma'aikatar albarkatun ruwa ta tarayya |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 47,754 | 49,621 | Hanya | Aiwatarwa | Haƙƙin ingantattun kayayyakin aiki | UDHR da Kundin Tsarin Mulkin ƙasa | 47,754 | 49,621 | Majalisar Karamar Hukumar, Ma'aikatar Kananan Hukumomi da Ma'aitar Ayuyyuka | |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 47,754 | 49,621 | Karancin Kayayya-kin amfanin gona | Wahalar samun takin zamani | Haƙƙin Ingantaccen abinci | | 47,754 | 49,621 | Majalisar Karamar Hukumar Gaya, Ma'aikatar Noma ta Jiha KEDCO, | Maza, Mata, Matasa da Yara |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 47,754 | 49,621 | Wutar lantarki | Aiwatarwa | Haƙƙin Ingantattun ababan more rayuwa | | 47,754 | 49,621 | Majalisar Karamar Hukumar Gaya, Ma'aikatar Kananan Hukumomi | |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 47,754 | 49,621 | Ruwa | Aiwatarwa | Haƙƙin ababan more rayuwa | | 47,754 | 49,621 | Majalisar Karamar Hukumar Gaya, Ma'aikatar Kananan Hukumomi da Ma'aikatar albarkatun ruwa | |





# KALUBALEN DA KE FUSKANTAR GARIN WUDILAWA A HALIN YANZU

Kalubalen dake fuskatar garin Wudilawa a halin yanzu sun haɗa da rashin ababan more rayuwa kamar wutar lantarki, asibiti, kyakykyawar hanyar mota, wadataccen ruwan sha, wadatattun kayayyakin aiki a makaranta, kayayyakin gona, matsalar ambaliyar ruwan sama da kuma ɗakunan koyan sana'o'i.

An jera matsalolin wannan garin ta hanyar tsarin na matsalar da tafi ciwa al'umma tuwo a ƙwarya a sama (duba jadawalin dake tafe). Al'ummar garin Wudilawa sunyi amannar cewa maganta matsalar ambaliyar ruwa a garin zai mutukar haɓaka rayuwar mazauna garin, ta yadda jama'a zasu shagaltu da sana'o'i daban-daban. Hakan kuma zai rage taɓarɓarewar tattalin arziki a garin dama yawan ci rani da jama'ar garin Wudilawa ke tafiya zuwa waɗansu garuruwan.

Rashin ingantaccen asibiti shi aka saka a matsala ta biyu. Samar da ma'aikatan lafiya da magani a asibiti da sauran kayayyakin aikin asibiti zasuyi mutuƙar rage mutawar mata masu juna biyu wajen haihuwa da ƙananan yara ta yadda mata ba sai sunyi tafiyar kilomita 25 wajen neman lafiyarsu ba. Rukunin jama'a guda uku aka tuntuba domin jin ta bakinsu akan waɗannan lammuran.

# SASSAUKAR **HANYAR JERAN MATSALOLI**

Domin faɗaɗa tantance matsalolin anyi amfani da sassauƙar hanyar Jeran matsaloli da matsaya kan yadda za a magance su.

| AL'AMARI (Buƙatu) | MATA | YARA | MAZA | ADADI | MATSAYIN (Buƙatun) |
|---|---|---|---|---|---|
| Tsabtaccen Ruwan Sha | 15 | 41 | 0 | 62 | Na 3 |
| Hanyar Mota | 35 | 23 | 0 | 58 | Na 4 |
| Lafiya | 11 | 21 | 0 | 32 | Na 6 |
| Ilimi: Buƙatar samar da makaranta da kuma gyaran makarantar garin | 42 | 120 | 156 | 369 | Na 1 |
| Rashin aikin yi | 23 | 4 | 0 | 27 | Na 7 |
| Wutar lantarki | 26 | 26 | 0 | 52 | Na 5 |
| Ambaliyar ruwa | 223 | 21 | 0 | 244 | Na 2 |
| Takin zamani | 4 | 20 | 0 | 24 | Na 8 |








# TANTANCE MATSALOLI TA AMFANI DA BISHIYAR MATSALOLI

Bishiyar matsaloli ta taimaka wajen tantance manyan matsalolin da ke addabar garin. Bishiyar hoto ne da ke nuna dangantaka tsakanin abubuwan da suka haddasa matsalolin da kuma tasirinsu. Bishiyar matsaloli tana buɗe ƙofar shiga tsakani tun daga tushen abubuwan da suka janyo ta da zummar warwarewa.

Don haka, tushen matsalar jama'ar wannan gari shi ne rashin magudanan ruwa, toshewarar hanyar ruwan kogi da ciyayi sukayi, rashin hanyoyin ruwa, tsofaffi da sababbin hanyoyin ruwanda suka tafi kogin, faɗaɗa gonaki, gini akan magudanan ruwa da kuma ƙona dajijjika. Ganyan bishiyar kuma shi yake nuni da abin da matsalar zata jawo waɗanda suka haɗa da asarar rayuka da dukiyoyi, ɓata makabartun garin, ɓata hanyoyin mota da hanyoyin kafa, taɓarɓarewar kasuwanci da zirga-zirgar ababan hawa da taɓarɓarewar sadarwa, da naƙasa tsarin karatu, da lalata gonaki da amfanin gona da da na kiwo dama yaɗuwar cututtuka idan ba a maganta ba kamar yadda aka tattauna da al'ummar Wudilawa, an nuna a bishiyar matsaloli da ke tafe.








# KUNGIYOYI DA MUTANEN DA ZA SU IYA TALLAFAWA

Abubuwan da suka taso daga bishiyar matsaloli, an yi nazarin ƙungiyoyi da mutanen da za su iya bayar da gudummawa wajen warware matsaloli. Al'ummar Wudilawa sun fitar da muhimman mutanen da suke da zarafin tallafawa domin samar da canjin da ake fata a garin.

## Jadawalin Tantance Matsaloli Garin Wudilawa

| ABUBUWAN DA AKA GANO | WAƊANDA ZA SU IYA TALLAFAWA | CIBIYOYI | MANYAN BUKATU/ ZABURARWA DOMIN KAWO CANJI | MATAKIN KARFIN IKON KAWO CANJI (SAMA TSAKA-TSAKI KO NA-KASA) |
|---|---|---|---|---|
| Ambaliyar Ruwa | 1.Mai Unguwa<br>2.Dagaci<br>3.Kansila<br>4.Liman<br>5.Shugaban Karamar Hukuma<br>6.Dan Majalisar Jiha<br>7.Sanata<br>8.Gwamna<br>9.Shugaban Kasa<br>10.Ɗan Majalisar Tarayya | 1.Karamar Hukumar Gaya<br>2.Gwamnatin Jihar Kano<br>3. HYRDA<br>4. Ma'aikatar Albarkatun Ruwa ta Tarayya<br>5. Ma'aikatar Kanan Hukumomi<br>6. Ma'aikatar Raya Karkara da Birane | 1.Cigaba<br>2.Cigaba<br>3.Siyasa<br>4.Cigaba<br>5.Siyasa<br>6. Siyasa<br>7. Siyasa<br>8. Siyasa<br>9. Siyasa<br>10. Siyasa | 1.Na Kasa<br>2. Na Kasa<br>3. Na Kasa<br>4.Tsaka-tsaki<br>5. Na Kasa<br>6. Tsaka-tsaki<br>7. Tsaka-tsaki<br>8.Sama<br>9.Sama<br>10. Tsaka-tsaki |
| 2.Ilimi; samar da Ajujuwa | 1.Mai Unguwa<br>2.Dagaci<br>3.Kansila<br>4.Liman<br>5.Shugaban Karamar Hukuma<br>6. Ɗan Majalisar Jiha<br>7. Sanata<br>8. Gwamna<br>9. Shugaban Kasa<br>10.Ɗan Majalisar Tarayya<br>11. Kwamishinan Ilimi<br>12. Kwamishinan Ayyuka | 1. Karamar Hukumar Gaya<br>2. Gwamnatin Jihar Kano<br>3. Ma'aikatar Ilimi<br>4. L.E.A<br>5. SUBEB | 1.Cigaba<br>2.Cigaba<br>3.Siyasa<br>4.Cigaba<br>5.Siyasa<br>6.Siyasa<br>7.Siyasa<br>8.Siyasa<br>9.Siyasa<br>10.Siyasa | 1.Na Kasa<br>2. Na Kasa<br>3. Na Kasa<br>4.Medium<br>5. Na Kasa<br>6. Tsaka-tsaki<br>7. Tsaka-tsaki<br>8. Sama<br>9. Sama<br>10. Tsaka-tsaki<br>11. Sama<br>12. Sama |
| 3.Ruwan Sha | 1.Mai Unguwa<br>2.Dagaci<br>3.Kansila<br>4.Liman<br>5.Shugaban Karamar Hukuma<br>6.Ɗan Majalisar Tarayya<br>7.Sanata<br>8.Gwamna<br>9.Shugaban Kasa<br>10.Ɗan Majalisar Tarayya<br>11.Kwamishinan Albarkatun Ruwa | 1. Karamar Hukumar Gaya<br>2. Gwamnatin Jihar Kano<br>3.Ma'aikatar Albarkatun Ruwa<br>4. HYRBDA<br>5. Ma'aikatar Kananan Hukumomi | 1.Cigaba<br>2.Cigaba<br>3.Siyasa<br>4.Cigaba<br>5.Siyasa<br>6. Siyasa<br>7. Siyasa<br>8. Siyasa<br>9. Siyasa<br>10. Siyasa | 1. Na Kasa<br>2. Na Kasa<br>3. Na Kasa<br>4. Tsaka-tsaki<br>5. Na Kasa<br>6. Tsaka-tsaki<br>7. Tsaka-tsaki<br>8. Sama<br>9. Sama<br>10. Tsaka-tsaki<br>11. Sama |



TANTANCE YANAYIN KARFIN IKO

An yi amfani da tsarin zane na Venn domin gudanar da wannan tantancewar. Haka kuma an yi amfani da tsarin zanen Venn domin tantance matakin ƙarfin ikon da wani mutum ko wata ƙungiyoyi ke da shi da kuma alaƙarsu da juna.

Karin Bayani: Zanen dake tafe ya fitar da mutane da cibiyoyi waɗanda suke da ikon warware al'amari ko matsalar da aka gano. Sanan kuma zanen ya nuna tazarar da mutane da cibiyoyin suke daga garin da kuma alaƙar su da juna.

Gwamnatin jiha nada tasiri sosai wajen kawo canjin da zai ciyar da al'u'mmar wannan gari gaba, haka kuma tana da alaƙa ta ƙud da ƙud da jama'ar garin. Haka kuma kwamatin raya karkara na jiha nada dama wajen kawo canji sai dai basu da alaƙa ta kai tsaye da jama'ar garin. Damar da Kansila da shugabanin al'umma keda ita ta kawo canji bata kai ta kawo ba duk da cewa su suka fi kusanci da al'ummar garin idan an kwatanta da shugaban ƙaramar hukuma wanda ke da tasiri sosai wajen kawo canjin da ake buƙata.

## TANTANCE MATSALOLIN DA KE ADDABAR GARIN WUDILAWA

Tantance matsaloli hanya ce ta gano da auna da kuma jera matsalolin da ke fuskantar garindaki-daki. Bugu da ƙari, an gano matsalolin da ke yiwa garin barazana. An yi amfani da jadawalin tantancewa wajen tattauna sabubban da suka haddasa su tare da tasirinsu.


| LAMBA | MATSALA | ABIN DA HADDASA MATSALAR | ABIN DA MATSALAR TA JAWO | TSAWON LOKACI | WAƊANDA SUKA FI CUTUWA |
|---|---|---|---|---|---|
| 1. | Ambaliyar Ruwa | Tumbatsar Kogi | Lalata gonaki, gidaje da dukiyoyi | Yadade yana faruwa | Kowa da kowa yara da manya |



KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN GARIN WUDILAWA 2016

Ta hanyar amfani da jadawalin matsaloli al'ummar garin sun fayyace irin ƙalubalen dake fuskantarsu a garin kamar matsalar rashin tsaro, ambaliyar ruwa da yaɗuwar Cututtuka.








# TANTANCE HANYOYIN SAMUN BAYANAI

Jama'ar garin Wudilawa na samun bayanai na abubuwan dake faruwa a wajen garin ta hanyar zantuttukan al'umma, Jaridu, Rediyo, Talabishin da Mai shela. Haka kuma suna musayar bayanai Da mutane da cibiyoyi ta hanyar wasiƙa da kuma saƙunan baka. Dagaci ko wakilinsa sune masu magana da yawun mutanen garin duk lokacin da buƙatara hakan ta taso.











# TSARIN DA AKA SHIRYA GUDANARWA NA AL`UMAR GARIN WUDILAWA

A ƙarshen tattaunawar, an fitar da ƙwaƙƙwaran tsarin da za a bi domin warware matsalolin da aka gano ta hanyar yin amfani da gudummawar kowa da kowa da wasu dabaru domin tantance abubuwan da ke ci wa al'ummar garin Wudilawa tuwo a ƙwarya. Abin da ke biye tsari ne na ayyukan da za aiwatar domin ganin mafarkin garin ya zama gaskiya.

| MAHIMMAN BATUTUWA | AIKIN DA AKA TSARA GUDANARWA | WAƊANDA SUKA ƊAUKI NAUYI | KAYAN AIKIN DA AKE BUKATA | MATSALOLI | SHAIDAR SAMUN NASARA | TSAHON LOKACI |
|---|---|---|---|---|---|---|
| Rangadi Don Saduwa Da Sauran Jama`a | Ganawar baka da baka | Yan kwamiti | Bayani game da wannan shiri | Lokaci | Rahoto | Sati 2 Satumba, 2015 |
| Daftarin cigaban unguwa | Gabatarwa da karɓar shawarwari | CITAD da al'ummar gari | Mutane | -Halin ko in kula daga gurin wasu jama'ar gari | Cikakken daftarin cigaban gari | 30 ga watan Nuwamba 2015 |
| Kaddamarwa | -Rarraba takardar gayata. -Hadin gwiwa da kafafen yada labarai ARTV -Shiri don tattaunawa | CITAD da al'ummar gari, Dattijai, Yan kwamiti da Kungiyoyin Matasa | Takardar Kungiya Zirga-zirga Tuntuba Manema Labarai | Rashin samun ƙwararrun mutane da Cibiyoyi | Lokacin ƙaddamar-wa aika takardar gayyata | Wata 3 |
| Ziyarar ƙarfafa gwiwa ga waɗanda nauyi ya hau kansu | Ziyarar ƙarfafa gwiwa | CITAD da al'ummar gari | -Al'ummar Gari - daftarin cigaban gari -Kafafen yaɗa labarai | Lokaci -Kayayyakin gudanarwa | | 30 watan Maris 2016 |